Kashi na 1
Alherin
Bayaswa

# Mene ne Bayaswa?

Darasi na 1



A KAN ME
AKE MAGANA?

A ƙarshen darasin nan ya kamata ɗalibai su:

- san muhimmancin bayarwa.
- gane abin da ya shafi bayarwar Kirista.
- kasance a bude domin bishewar Allah game da bayarwa.

ME NAKE
BUKATA?

- su L.M.T.
- littafin rubuta matuni da biro
- shirya su tambayoyi domin lokacin tattaunawa a waƙoƙi 2 dabam - dabam.

AYYUKAN SHAKATAWA! MINTI 10

## Bayaswa Kulawa ce!

**Jagua** ya bar gida da naira ashirin kawai cikin aljihunsa. Tun da yake ba shi da keken hawa dole ya yi tafiyar km 3 da kafa zuwa wurin aikinsa. Da juyawa kwana kawai sai ya ga wani fakiri makaho mai bara cikin matsananciyar bukata. Yana da zazzabi kuma yana bukata a kai shi dakin magani. Cikin hanzari Jagua ya tsai da taksi kuma ya ba direbar naira ashirinsa don ya kai mai barar dakin magani.

Ba da jimawa ba Jagua ya tuna da naira ashirinsa sa'ad da lokacin cin abinci ya yi. I, da wannan zai saya masa abinci mai yawa, amma da ya yi tunanin mai bara nan sai ya yi farin ciki don ya iya taimakawa a kai shi dakin magani.

**Gabriel** Kwamishona ne na Gwamnatin Jiha. Ya tafi ƙauye don ya halarci kad-amawar asusun ginin sabon rijiya domin jama'a. An ba shi wuri mai daraja a wajen bikin sa'an nan sa'ad da lokaci ya yi sai ya ba da nasa kuɗin taimako mai tsoka yayin da mutane ke ta tafawa sosai.

1. Kowace ƙyauta da an bayar don taimakon kyautata rayuwar mutane ne. Kyautar tsokar kuɗi ya fi na naira ashirin?
2. Mene ne ya iza:
   a. Jagua don ya bayar?
   b. Gabriel don ya bayar?

YI MAGANA A KAI MINTI 15

## Bayarwa irin ta Kirista

**B**ayarwar Kirista na da muhimmanci don dalilai uku. Ko ka iya saninsu?

**1. Alamar sujada ce.**

Yayin da muke bayar da kyautan kuɗinmu ko sauran abubuwa muna ba da kanmu ne ga sauran mutane. Wannan aikin hidima ga waɗansu aikin sujada ce ga Allah.

**2. Bayyana godiya ce ga Allah saboda abin da ya yi mana.**

Mun sami kyautar Sabon Rai daga wurin Ubangiji. Kyauta ce ta sa dalilin mutuwar Yesu don mu sami yanci daga nauyin zunubanmu. Ba da kyautar kuɗi ko kaya ko taimako ga waɗansu wata hanya ce ta nuna godiya ga Yesu saboda dukan abin da ya yi dominmu.

**3. Shelar bangaskiya ne.**

Bayarwa don muna so mu bayyana ƙaunarmu domin waɗansu wata hanya ce da ke nuna cewa mun gane da abin da ake nufi da samun kyautar ceton Allah. Muna samun kyautar ƙaunar Allah ta wurin Yesu don mu iya nuna wannan ƙauna ga waɗansu.

KU DUBA LITTAFIN! MINTI 20

# Misali mafi kyau!

K**aranta Afisawa 4:32-5:2**

1. Wane dalili ne Bulus ke bayarwa cewa ya kamata mu kula game da waɗansu kamar yadda Allah ke yi?

2. Ba da misalai biyu na abin da kake tsamani ake nufi da "ku yi zaman ƙauna" (aya 2)?

3. Waɗanne irin hanyoyi ne Yesu ya nuna mana misalin ƙauna da za mu bi?

4. A wace hanya ta musamman ne Yesu ya nuna mana ƙaunarsa? Akwai yadda za mu yi koyi da shi?

**Karanta Yahaya 3:16** (Idan ba ka san shi sosai ba).

5. Me Ubangiji ke ce mana a cikin ba mu wannan kyauta ta musamman na Ɗansa tilo? Ga wa aka ba da wannan kyauta?

6. Yaya za ka yi da wannan kyauta?

**Karanta 2 Korantiyawa 8:1-4**

7. Me ake nufi da 'alherin' da Allah ya ba mutane a waɗannan majami'un Helinawa na Makidoniya?

8. Yaya wannan 'alherin' ya shafi hanyar da suka yi tunani game da bukatun waɗansu?

9. Menene halin da suka nuna game da wannan hidimar bayarwa (aya 4)?

10. Me kake tsammani waɗannan ayoyi kima na faɗi game da albarkun da sun samu sakamakon yalwar ban gaskiyarsu?

AYYUKAN AIKATAWA MINTI 15

# Kyautar Ruwa...!

Ku rabu ƙungiya biyu domin ku tattuna tare na minti 10. Kowace ƙungiya ta za€i shugabanta. Ku kuma zaɓi sakatare don ɗaukan muhimman abubuwa cikin tattunawarku.
Bayan minti 10 sai ku haɗu ku faɗi muhimman abubuwan.
Ku bar mutum ɗaya daga kowace ƙungiya ya yi tambaya wanda ya taso daga tattunawar ɗayan ƙungiyar.

**Ƙungiya ta 1.**

1. Ko kana tsammani Jagua ko Komishina Kirista ne? Ba da dalilai domin amsarka.
2. Da me za ka yi in kana irin halin Jagua? Don me?

**Ƙungiya ta 2.**

1. Lissafa a kalla abubuwa 10 da Allah ke ba mu kyauta. Don me ka ji Allah na ba mu waɗannan abubuwa?
2. Ban da cewa Allah na gode, ka yi tunanin wata hanya da za ta nuna godiyarka ga Allah domin ɗaya daga cikin wadannan kyautai.

**Sujada**
Mori sauran 'yan mintocin da sun ragu cikin yin yabo da sujada, kuna gode wa Allah domin yawan albarkunsa zuwa gare ku.

Roƙe Allah domin ya ba ka alherin bayarwa ga masu bukata.

AIKIN GIDA NA WANNAN MAKO:

- Rubuta Yahaya 3:16 a ka.
- Sai ka rubuta abin da za ka yi da kyautar da Allah ya ba ka.
- Ta wace hanya ne za ka nuna wa Allah godiya don wannan ƙyautar?
- Kafin mako mai zuwa ka tambayi :

a) membobi uku a cikin jama'a da

b) membobi uku a ikiiisiya dalilin da ya sa suke yin kyauta ko baiko.

Ka rubuta amsoshin -su don ka faɗa wa ƙungiya mako mai zuwa.